Lallai akwai halayyar daji ga wadannan dabbobin kamar dabbobin daji, wanda ya bijere muku daga cikinsu to ku yi haka da shi'

Daga rafi'u ɗan Khadij - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Mun kasance tare da Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - a Zul-hulaifa, sai yunwa ta kama mutane, sai suka samu raƙuma da tumakai, ya ce: Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya kasance yana cikin ƙarshen mutane, sai suka yi gaggawa, suka yanka, suka girka tukwane, sai Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya yi umarni da tukwane, sai aka kifar da su, sannan ya raba, sai ya daidaita tumakai goma da raƙumi ɗaya sai wani raƙumi ya yi tsaurin kai, sai suka neme shi, sai ya gajiyar da su kuma a cikin mutanen dawakan kaɗan ne, sai wani mutum daga cikinsu ya sunkuyar da kibiya, sai Allah Ya tsare shi, sannan ya ce: "Lallai akwai halayyar daji ga wadannan dabbobin kamar dabbobin daji, wanda ya bijere muku daga cikinsu to ku yi haka da shi'. Sai ya ce: wato rafi'u: Lallai mu muna jin kwadayi - ko muna jin tsron - makiya gobe, kuma babu wuka a tare da mu, shin zamu yanka ne da kara? ya ce: "Duk abinda ya zubar da jini, kuma aka ambaci sunan Allah akansa to sai ku ci shi, banda hakori da farce, kuma zan zantar da ku game da haka: Amma a hakori to kashi ne, amma farce to wuƙar mutanen Habasha ce".

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Rafi'i ɗan Khadij - Allah Ya yarda da shi - ya bada labarin cewa su sun kasance tare da Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - a Zul-Hulaifa, sai yunwa ta kama mutane, alhali sun samu ganimar raƙuma da tumakai daga mushrikai, sai suka yi gaggawa kafin raba ganima sai suka yanka wasu daga cikinsu, kuma suka kafa tukwane, ba tare da sun nemi izinin Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ba, kuma (Annabi) tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya kasance yana tafiya a cikin ƙarshen mutane, lokacin da (Annabi) tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ya sani sai ya yi umarni da tukwanan, sai aka kifar da su da abinda ke cikinsu na miya, sannan ya raba ganimar a tsakaninsu, sai ya sanya goma daga cikin tumakai a madadin rakumi daya, sai wani rakumi ya gudu daga cikinsu, sai suka kasa kama shi, kuma dawakan sun kasance kada ne, sai wani mutum ya harbe shi da kibiya, sai Allah Ya tsare musu shi, sai (Annab) tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ya ce: Lallai akwai wasu ɗabi'u kamar ɗabi'un daji ga waɗannan dabbobin masu sabo, wanda ya rinjayeku daga cikinsu kuma kuka kasa kama shi to ku yi haka da shi. Sai Rafi'u ya ce: Lallai mu mana fatan fuskantar maƙiya gobe, kuma muna jin tsoron yankanmu ga dabbobin ya cutar da makamanmu alhali ana tsananin buƙatar yanka, kuma babu wuka a tare da mu, shin zamu yanka ne da busassun karare? Sai (Annabi) tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ya ce: Duk abinda ya zubar da jini kuma ya kwaranyar da shi da yawa, kuma aka ambaci sunan Allah a kansa to ku ci shi, banda haƙori da farce, kuma zan zantar daku game da hakan: Amma haƙori to ƙashi ne, amma farce to mutanen Habsha kafirai ne

suke amfani da shi.